# Idan dayan ku ya tashi zai yi sallah, to ya sanya Sutura idan akwai a gabansa gwargwadon Karshen Siddin Doki yaya, kuma idan babu a gabansa Karshen Sirdin Doki, Saboda Jaki da Mace da Bakin Kare za su iya katse Sallarsa.

Daga Abu Dharr - Allah ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah -SAW- ya ce: “Idan dayan ku ya tashi zai yi sallah, to ya sanya Sutura idan akwai a gabansa gwargwadon Karshen Siddin Doki yaya, kuma idan babu a gabansa Karshen Sirdin Doki, Saboda Jaki da Mace da Bakin Kare za su iya katse Sallarsa», sai na ce: Ya Abu Zarr, menene matsalar baƙin kare ko jan kare ko rawaya? Ya ce: Ya dan dan uwana, na tambayi Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - kamar yadda ka tambaye ni, sai ya ce: “Bakin kare shaidan ne.” Kuma a cikin wata ruwaya daga hadisin Ibnu Abbas - Allah ya yarda da su - cewa: "Mace mai haila da kare za su bata sallah."

[Ingantacce ne] [Abu Daud Ya Rawaito shi - Muslim ne ya rawaito shi]

Idan mai Sallah ya tsaya a cikin sallarsa, to ya yi Sutura domin sallarsa, mafi girman ta ya zuwa bayan Sirdi, kuma ya zama kashi biyu cikin uku na hannu da zai sanya a gabansa, kuma idan ya bai yi ba tp zai iya bata sallarsa daya daga cikin abubuwa nan uku: mace, kuma an kebance ta a cikin hadisin Abu Dawud da mai jinin Haila watau Babba, jaki, da baƙin kare Idan ya sa sutura a gaban shi, ba zai cutar da shi ba, koda kuwa yana ɗaya daga cikin ukun nan sun ratsa. Abdullahi bn Al-Samit, wanda ya ruwaito hadisin, ya ce: Na ce: Ya Abu Dhar, me ya sa bakar kare ta jan kare ta fi karen rawaya? Wato, me yasa aka yi amfani da wannan kare kawai don yanke sallah ba sauran karnukan ba? Ya ce: Ya dan dan uwana, na tambayi Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - kamar yadda ka tambaye ni, sai ya ce: “Bakar kare ka ce aljan.” Abin da ake nufi da katse Sallah shi ne rashin ingancinsa, kuma a kan haka ne zaunannen kwamitin ya bayar da fatawoyi, kuma wasu malamai suna ganin cewa tana katse girmamawarta da kamalarta, ba wai salla ta zama ba ta da inganci ba.